(١)

## KWANTAR DA HANKALI A CIKIN ALKUR'ANI MAI GIRMA

Godiya ta tabbata ga Allah Ubangijin talikai, wanda a cikin littafinsa mai girma yake cewa: **(Kuma lallai mun san cewa kana matuƙar damuwa da abubuwan da suke faɗi, kada ka damu da su, kai dai kawai ka tsarkake Ubangijinka, ka gode masa, ka zama cikin masu miƙa masa wuya, ka bauta wa Ubangijinka har ajali ya riske ka)** [al- Hijr: 97- 99]. Ina shaida cewa lallai babu abin bauta wa da gaskiya sai Allah shi kaɗai, ba shi da abokin tarayya. Ina kuma shaida cewa lallai shugabanmu, kuma Annabinmu Muhammad bawan Allah ne kuma Manzonsa, Ya Allah Ubangiji ka ƙara masa tsira da aminci da albarka, shi da alayensa da sahabbansa, da duk wanda ya bi tafarkinsu da kyautatawa har zuwa ranar sakamako, Bayan haka:

Lallai kwantar wa mutane da hankula na cikin manyan ɗabi'un Musulunci masu girma, da ma manyan ɗabi'un mutuntaka masu falala da mutum yake taimaka wa waninsa, ta yanda zai yi galaba akan baƙin- ciki, da raɗaɗin da suke damunsa, lallai duk wanda zai yi wa littafin Allah duba na lura zai ga irin yanda ya bai wa wannan ɗabi'a ta kwantar da hankula kulawa ta musamman, kai hasali ma Allah Maɗaukakin Sarki ne da kansa yake kwantar wa Annabawa, da waliyyai, da zaɓaɓɓun da ya zaɓa da hankulan, ga shugaban halitta (SallalLahu alaiHi wa alihi wa sallam) nan, lokacin da mutanensa suka cutar da shi, bai kuma sami komai daga gare su ba banda kawar da kai, da juya baya, sai Allah ya kwantar masa da hankali a inda yake cewa: **(Ka yi haƙuri da abin da Ubangijinka ya hukunta, lallai kana ƙarƙashin kulawarmu..)** [al- Ɗur: 48], ma'ana ka yi haƙuri da juriya da abin da Ubangijinka ya hukunta cikin abin da ya ɗaura

maka na isar da saƙonsa, da ma abin da Allah ya jarabce ka da shi, da yake zuwa daga mutanenka, lallai kana ƙarƙashin kulawa da sanya idonmu, za mu ba ka kariya, mu tsare ka.

Haka ma lokacin da zuciyarsa ta damu, ta kusa ta fashe saboda irin yanda ya damu; sakamakon kawar masa da kai da mutanensa suka yi, da ƙin amsar kiran gaskiya, Allah Ubangijinmu mai girma da ɗaukaka ya kwantar masa da hankali a inda yake ce masa: **(Lallai kai ka kusa ka halakar da kanka saboda baƙin cikin ba su yi imani da wannan Alƙur'ani ba)** [al-Kahfi: 6], da inda mai girma da ɗaukaka yake cewa: **(Lallai ka kusa ka halakar da kanka saboda ba su yi imani ba)** [as-Shu'ara'i: 3], ma'ana: Ta fa yiwu ka halakar da kanka saboda baƙin cikin sun juya wa gaskiya baya, lallai ire- iren waɗannan ayoyin sun sauka ne saboda su kwantar wa Annabinmu (SallalLahu alaiHi wa alihi wa sallam) da hankali, su kuma rarrashe shi (SallalLahu alaiHi wa alihi wa sallam).

Haka ma Ubangijinsa mai girma da ɗaukaka ya kwantar masa da hankali, a lokacin da ya nemi da kada ya ɗaura wa kansa sama da abin da ya fi ƙarfinsa, Allah Maɗaukakin Sarki yana cewa: **(Naka kawai shi ne isar da saƙo, shi kuwa hisabi aikinmu ne)** [ar- Ra'ad: 40], mai girma da ɗaukaka yana cewa: (**Kai ba mai yi masu dole ba ne**) [al- Gashiya: 22], kada ka ɗaura wa kanka abin da zai wahalar da kai matuƙa, ai aikinka shi ne isar da saƙo gami da bayani, ita kuwa shiriya da samun dacewa na Allah ne shi kaɗai, Allah Maɗaukakin Sarki yana cewa: **(Lallai kai ba ka shiryatar da wanda kake so, Allah ne yake shiryatar da wanda ya ga dama; saboda shi ne ya san su wane ne ya cancanci shiriya)** [al- Ƙasasi: 56].

Haka ma wanda yake yi wa Alƙur'ani mai girma kallo na tsanaki, zai ga inda Allah mai girma da buwaya yake kwantar wa da mahaifiyar Annabi Musa (AlaiHis Salam) da hankali, lokacin da ya ba ta umurnin ta jefa ɗanta a cikin kogi, zuciyarta ta tsinke matuƙa; saboda tsoron kada wani abu ya same shi, sai Allah mai girma da buwaya ya kwantar mata da hankali da cewa: **(Sai muka yi wa mahaifiyar Annabi Musa (AlaiHis Salam) wahayin ilhama, na ta shayar da shi, idan kin ji tsoron kada wani abu ya same shi, to ki sanya shi a cikin akwati, ki jefa shi cikin kumfar kogi, kada ki ji tsoro, kada kuma ki yi baƙin ciki, lallai mu ne za mu dawo maki da shi, mu kuma sanya ya zama cikin manzannin da za mu aike su)** [a- Ƙasasi:7], sannan ma haka Allah ya kwantar mata da hankali lokacin da ya dawo mata da ɗanta cikin karamci, Allah yana cewa: **(Sai muka dawo da shi zuwa ga mahaifiyarsa; saboda ta sami natsuwa, kada kuma ta yi baƙin ciki, saboda kuma ta sani cewa lallai alƙawarin Allah gaskiya ne, amma dai mutane mafi yawa ba su san haka ba)** [al-Ƙasasi: 13].

Haka ma a cikin Alƙur'ani mai girma bayanin kwantar da hankalin da aka yi wa Sayyida Maryam (AlaiHas Salam) ya zo, a lokacin da al'amurra suka yi mata tsanani, har ta kai ga cewa: **(Kaico na, ina ma a ce na rasu kafin wannan abu ya faru, mutane tuni sun manta da ni?!)** [Maryam: 23], sai Allah ya bayar da umurni a kira ta a kwantar mata da hankali, Allah Maɗaukakin Sarki yana cewa: **(Sai aka kira ta ta ƙarƙashinta cewa: kada ki yi baƙin ciki, lallai Ubangijinki yana halitta miki wani ɗan ƙaramin kogi a ƙasan inda kike, ga kuma bishiyar dabino nan ki girgiza ta za ta faɗo maki da ɗanyen dabino, ki ci,**

**ki kuma sha ruwan wannan ƙaramin kogin, ki kwantar da hankalinki..)** [Maryam: 24 – 26].

***

Godiya ta tabbata ga Allah Ubangijin talikai, tsira da aminci su tabbata ga cikamakin Annabawa da Manzanni, shugabanmu Annabi Muhammadu (SallalLahu alaiHi wa alihi wa sallam) da alayensa da sahabbansa baki ɗaya.

Lallai hanyoyi, da surorin kwantar da hankula suna da yawa, a cikinsu akwai: kwantar da hankali ta hanyar bayar da kuɗi, da kwantar da hankali ta hanyar nasiha, da kwantar da hankali ta hanyar yin tarayya na zuciya, da kwantar da hankali ta hanyar yin addu'a, lallai Alƙur'ani mai girma ya ambata mana kwantar da hankalin da mutumin kirkin nan ya yi wa Sayyiduna Musa (AlaiHis Salam), lokacin da ya fita daga cikin jama'ansa a tsorace, ya ba shi labarin abin da ya gudana tsakaninsa da Fir'auna, sai ya cewa: **(Kada ka ji tsoro, lallai ka tsira daga azzaluman mutane)** [al- Ƙasasi: 25], haka ma Alƙur'ani mai girma ya ambata mana kwantar da hankali da mala'iku suka yi wa Annabi Luɗu (AlaiHis Salam), lokacin da ya ji tsoron mutanensa, suka ce masa: **(Kada ka ji tsoro, kada kuma ka yi baƙin ciki, lallai mu ne za mu tseratar da kai da iyalanka..)** [al- Ankabut: 33]

Lallai Allah ya ba wa Annabinmu (SallalLahu alaiHi wa alihi wa sallam) umurni na ya sifantu da wannan sifa mai daraja, shi ya sanya Annabinmu (SallalLahu alaiHi wa alihi wa sallam) yake cewa: **(Duk wanda yake da abin hawa bayan abin hawansa, to ya bayar da shi ga wanda ba shi da abin hawa, haka ma duk wanda yake da guzuri da ya wuce buƙatarsa, to ya taimaka wa wanda ba shi da guzuri)**, haka ma (SallalLahu alaiHi wa alihi wa

sallam) yana cewa: **(Wanda yake son Allah ya tseratar da shi daga baƙin cikin ranar alƙiyama, to ya yaye wa mara shi, ko ya sauke masa damuwarsu)**, haka ma (SallalLahu alaiHi wa alihi wa sallam) yana cewa: **(Allah ba zai gushe wajen biya wa bawansa buƙata ba, matuƙar shi bawan ya tsaya wajen biya wa ɗan uwansa buƙatarsa)**.

Lokacin da Annabinmu (SallalLahu alaiHi wa alihi wa sallam) ya sami tabbata a garin Madina, mutanen Makka al- Muhajirun sun zo suka ce: ya Manzon Allah, ba mu ga mutanen da suke yawan ciyarwa, ko masu kyautata kwantar da hankali a cikin abu kaɗan da aka samu kaman mutanen da muka sauka a cikinsu ba –suna nufin al- Ansar (Allah ya ƙara yarda da su)-, haka ma (SallalLahu alaiHi wa alihi wa sallam) ya yabi ƙabilar Ash'arawa saboda sun sifantu da wannan sifar a lokacin da yake cewa: **(Lallai idan abincin ƙabilar Ash'arawa ya ƙare a wurin yaƙi, ko abincin iyalansu ya yi ƙaranci a garin Madina, sukan haɗa duka abin da ya rage masu a wuri ɗaya, sai su sake raba shi a tsakaninsu daidai wa daidai, lallai su mutane na ne, ni ma nasu ne)**.

Lallai mutana matuƙar buƙatar mu sifantu da sifar kwantar wa junanmu da hankula; saboda ruhin 'yan uwantaka ya yaɗu a tsakaninmu, dangantaka tsakanin al'umma kuma ta ƙara ƙarfi, haɗin kai da soyayyar juna su sami wurin zama a cikinsu.

**Ya Allah Ubangiji ka haɗa kawunanmu, ka kuma daidaita tsakaninmu.**